

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Tare da Allah Har abada

Yesu ya mutu domin mu kasance tare da Allah har abada



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Bangare na uku na rayuwar da muke da ita a cikin Kristiita ce cikar aikin Yesu na har abada— rayuwa ta har abada a gaban Allah maimakon jefar wa cikin jahannama har abada.

> "Domin Ubangiji kansa ma zai sauko daga sama da kira mai ƙarfi, da muryar babban mala'ika, da kuma busar ƙahon Allah. Waɗanda suka mutu suna na Kristi su ne za su fara tashi. Sa'an nan sai mu da muka wanzu, muke a raye, za a ɗauke mu tare da su ta cikin gajimare mu sadu da Ubangiji a sararin sama. Sai kuma kullum mu kasance tare da Ubangiji." (1 Tassalunikawa 4:16–17)

Karshen fansa shi ne zama na har abada a gaban Allah. Surori biyu na ƙarshe na Wahayin Yahaya sun bayyana zamanmu na har abada a gaban Allah:

> "Sa'an nan na ga sabuwar sama da sabuwar ƙasa, don sama ta farko da ƙasa ta farko sun shuɗe. Ba kuma sauran teku [babu sauran rabuwa, babu sauran ɗacin rai]. Sai na ga tsattsarkan birni, Sabuwar Urushalima, tana saukowa daga sama daga wurin Allah, shiryayyiya kamar amaryar da ta yi ado saboda mijinta." (Wahayin Yahaya 21:1–2)

Na gaskata cewa Sabuwar Urushalima ita ce Ikkilisiya mai saukowa daga sama. Kuma mazaunin Allah ne na har abada. Ɗaya daga cikin manyan manufofin Allah a cikin Ikkilisiya shi ne samun wurin da zai zauna har abada. Aya ta 3 ta ce:

> "Na kuma ji wata murya mai ƙara daga kursiyin tana cewa: 'Kun ga mazaunin Allah yana tare da mutane, zai zauna tare da su, za su zama jama'arsa. Allah kuma shi kansa zai kasance tare da su.'"

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa zan rayu har abada a gaban Allah maimakon a jefar da ni, domin Yesu mutu domin in saɗu da Allah har abada. Amin.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-150-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources

